# HARSHEN FULATANCI SHINE KAN GABA A WAJEN YADA ADININ MUSULUNCI DA FANNONIN ILIMI A DAULAR USMANIYYA

**DAGA**

**IBRAHIM JUNAIDU SOKOTO**

**Takardar Da aka gabatar a taron**
**Kara Wa Juna Sani A Bukukuwan**
**Shekara dari biyu Da Kafa Daular Musulunci**
**Ta Sakkwato,**
**Wuri: Makarantar Alkur'ani maigirma**
**ta Dr Attahiru Bafarawa, Sakkwato,**
**Daga 23 – 25, Yuli 2004.**

Bismillahi Rahmanir Rahim

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah Madaukakin Sarki. Tsira da amincinSa su tabbata ga Annabinsa Muhammadu (SAW) da Alayensa da wadanda sunka yi koyi dasu har zuwa ranar kiyama.

Assalamu Alaikum,

Manufar rubuta wannan takarda shine bada takaitaccen bayani akan irin rawar da harshen Fulatanci ya taka a wajen yada Addinin Musulunci da kuma yada fannonin ilimi daban daban a cikin wannan daula ta Usmaniyya.

Hakika, Shehu Usmanu R.A. da mataimakansa sun zuba fannonin ilimi daban daban a cikin wakokin su na Fulatanci kuma sun yi bayani kwatta-kwatta a cikinsu fiye da bayanin da suka yi a cikin rubuce-rubucensu na larabci, dalili kuwa mafi yawan jama'ar wancan lokaci nasu jahillai sun fi yawa.

Kafin in shiga bayani a kan abinda wannan takarda zata yi bayani, ina son inyi kira ga dalibbai masu kwazo da su tashi tsaye su yi muna binciken wadannan wakokin Fulatanci da Shehu Usmanu da mataimakansa suka rubuta muna domin su zakulo muna wadannan fannonin ilimi domin amfanin Al'umma baki daya.

Alhamdu Lillahi, a yanzu ana karatun wannan harshe na Fulatanci a Kolejin Ilimi ta Shehu Shagari dake nan Sakkwato. Hakika ba karamin taimako ne wannan Kolejin ta yi ba na sanya karatun wannan harshe a cikin tsarin kwasakwassan da take gudanarwa ba don rayar da wannan harshe mai albarka. Domin a halin yanzu ana karatun share fage na takardar shaida ta kasa (Pre-N.C.E.) a cikin wannan harshe na Fulatanci. Allah Shi kara daukaka wannan makaranta shi kuma taimaki shuwagabanninta da suka yi nazari suka sanya wannan karatu

a cikin tsarin kwasakwassansu. Allah kuma Shi kara taimakon Gwamnatin jihar Sokoto ga dukkan al'amurranta na ci gaban wannan jiha da kuma kasa baki daya akan yarda da kuma amincewar da tayi akan gudanar da tsarin karatun wannan harshe mai albarka a cikin wannan babbar makaranta.

Bari mu komo a kan abin da wannan takarda zata yi bayani a kai.

1. Dangantakar Harshen Fulatanci da Addinin Musulunci tare da bada takaitaccen bayani a kan asalin Fulani
2. Halayen Mutanen kasar Hausa kamin bayyanar Shehu Usmanu da irin hanyar da yabi ya risba wadannan miyagun halaye.
3. Sashen Rubuce-Rubucen Shehu Usmanu R.A. na Fulatanci a fannonin Ilimi daban-daban.
4. Illolin dake cikin rashin bincike a cikin rubuce-rubucensa na Fulatanci da na mataimakansa a wajen rubuta tarihi ko gudummuwarsu ga Daular Usmaniyya.

## DAGANTAKAR HARSHEN FULATANCI DA ADDININ MUSULUNCI TARE DA BADA TAKAITACCEN BAYANI A KAN ASALIN FULANI

Mutane da dama suna jin ana ambaton harshen Fulatanci amma basu san irin dangantakar wannan harshe ba ko Al'ummar wannan harshe zuwa ga Addinin Musulunci ba musamman a wannan daula ta Usmaniyya. Wasu ma idan suka ji an ambaci Fulani ba zasu daukesu da wata daraja ba, sun daukesu kawai mutanen daji ne.

Abin ma takaici har a cikin Fulanin akwai wasu jahilai dake ganin sunyi karatun zamani basu ko son a kira su Fulani in kuma har suna jin harshen fulatanci ba zasu so suyi magana dashi ba saboda a ganinsu tunda sun yi karatun zamani sun shigo birni wai harshen Fulatanci kauyanci ne. Saboda rashin sanin darajar wannan harshe zuwa

garesu da kuma darajarsa ga Addnin Musulunci. Saboda haka naga ya kamata a cikin wannan takarda in dan ambaci dangantakar wannan harshe mai albarka zuwa ga Addinin Musulunci saboda irin rawar daya taka a wajen yada addinin Musulunci da kuma fannonin ilimi daban-daban a cikin wannan daula ta Usmaniyya.

Harshen Fulatanci wani harshe ne ko yare na wata shahararrar Al'umma madaukakiya daga cikin shahararrun Al'ummomin duniya wadda tayi anfani da harshenta ta jaddada addinin Musulunci da fannonin Ilimi daban daban a cikin wannan kasa tamu ta Hausa a karkashin shugabancin Shehu Usmanu Foduye (R.A.) wanda shike shine musabbin kafuwar wannan daula ta Usmaniyya Jama'ar wannan kabila ana kiransu "Fulani"

Har zuwa yau, marubuta tarihi basu bada tabbatacen inda wannan kabila ta Fulani ta fito ba.

A wani kauli an ce wannan kabila ta Fulani dama kabila ce dake zaune a cikin kasar Senegal, daga baya suka bazu cikin Sudan saboda su sana'arsu wancan wuri suna nemarwa dabbobinsu wurin kiwo[1].

A wani kauli kuma ance daga Yahudu suka fito a wani kauli kuma ance daga Nasara[2]

Amma kaulin da yafi karbuwa musamman a wurin magabatan malaman mu shine, Fulani sun fito ne daga Duri Sina dake cikin kasar Sham suka biyo ta gefen Arewa na Afirika ta yamma har suka sadu da garin Futa suka zauna a nan. Anan ne Uqbatu bn Nafi'i ya sadu da su Sa'ad da yazo da rundunar yaki zuwa Afirka don jaddada addinin Allah a zamanin sarki Umar Ibn Al Asi sai suka shiga Musulunci bada yaki ba. Lokacin nan ne Uqbatu ya auri diyar Sarkinsu wadda ake kira

Bajjo Manngu, har suka haifi 'ya'ya hudu sune Deita, Nasi, Woya da Roroba. Wadannan sune asalin dukan Fulani.

A kwana a tashi zuriar wadannan 'ya'ya guda hudu suka yawaita suka warwatsu cikin duniya har sahshen su suka iso wannan kasa tamu ta Hausa a cikin shekara ta 500 AH a karkashin jagorancin Musa Jakollo wanda shine kakan Shehu Usmanu Dan Foduye na 12 suka sauka a konni wadda a halin yanzu ke cikin jamhuriyar Nijar.

Saboda rashin kwanciyar hankali tsakanin su da Sarkin Konni Demka sai suka kasu biyu sannan dukansu suka tashi daga Konni, kashi daya ya sauka a Kuluba kashi na biyu kuma ya sauka a garin Maratta [3], wato garin da aka haifi Shehu Usmanu a shekarar 1168 AH 1754 AD shike shine ya shugabanci yakin jihadin jaddada Addinin Musulunci a kasar nan ta Hausa wanda shike kuma shine sanadiyyar kafuwar daular Musulunci a wannan kasa tamu.

**HALAYEN MUTANEN KASAR HAUSA KAMIN BAYYANAR SHEHU USMANU R.A.**

Mutanen kasar Hausa kamin bayyanar Shehu Usmanu R.A. sun kasu kashi uku.

Kashi biyu daga cikin kashi ukku din nan duka kafirrai ne [4] sa'annan kuma mutanen bidi'a sun rinjayi malamansu.

A cikin infaq Al-Maisuri, sarkin Musulmi Muhammadu Bello ya ambata cewa, sarakunan kasar Hausa, mayakansu da miyagun malaman su suna hada aikin Musulunci da kafirci amma duk da haka suna da'awar musulunci ga kanunsu, gasu kuwa suna kalmar shahada sallah da azumi amma kuma suna hadawa da wasu ayyuka da ba'a samunsu

sai ga kafirrai. Kamar jahiltar abinda ke walwale imani. Misali yanke-yanke ga itace da duwatsu da musun gaskiya wadda take bayyana daga cikinsu har akwai masu ikirari da kafirci [5].

Ta bangaren malaman kasar Hausa kuwa Shehu Usmanu R.A. yayi bayaninsu a cikin wakarsa ta Fulatanci mai suna Yimre Tsamiya cewa kashi biyu suke kashi daya sunyi karatu sunyi aiki da shi sun kuma koyar da jama'a sun kuma hore su da suyi aiki da shi. Kashi na biyu kuwa sunyi karatu amma basu yi aiki da shi ba basu koyar ba kuma basu yi horo ayi aiki dashi ba kashi na ukku kuwa sun yi amma wurin koyarwa da kuma wurin horon jama'a suyi aiki da karatun sai suna tsanantawa [6]

A cikin wakkokinsa na fulatanci, Moodinoore (mai ilmantarwa) Yaynotoode (mai haskakawa) Shehu Usmanu yayi bayanin irin miyagun halayensu wadanda suka saba ma Musulunci wadanda suka hada harda girmama al'adunsu da suka saba ma Musulunci fiye da Addinin Musulunci kamar bori, tsafe-tsafe, bugun kasa, bokanci, garwayar maza da mata a kasuwanni da lokuttan bukukuwansu. Haka kuma suna yin sallah ba tare da alwala ba basu rabon gado kuma suna wuce masana ga sharia, matansu basu lullubi basu kuma karatu da dai sauransu.

Saboda lura da irin miyagun halaye na sarakuna, malamai da kuma mutanen kasar Hausa, Shehu Usmanu (R.A.) yayi tsaye tsayin daka ya horar da almajiransa hanyoyin da zasu bi kawar da wadannan miyagun al'adu. Saboda abin daya fara kokarin yi shine tabbatar da samun malamai managarta wadanda zasu taimaka masa wurin kawar da wadannan miyagun al'adu. Saboda a nasa ganin tabbatar da cewa idan aka samu malaman kirki na gari a cikin kasa sai mutanen kasar

su zamo masu kirki, al'amarin kasar shi yi kyau kuma kasar tayi lafiya. Idan kuma aka samu miyagun malamai a cikin kasa sai mutanen kasar su baci kuma al'amarin kasar shi baci [7]

To bayan Shehu Usmanu R.A. ya horarda almajiransa sai ya fito tare da su suka fara wa'azi suna kyamatar da wadannan miyagun al'adu ta hanyar wakokokinsa na Fulatanci [9] har Allah Ya basu ikon risbe wadannan miyagun al'adu a kasar Hausa suka kuma kafa wannan daula ta Musulunci da kuma fannonin ilimi daban daban a cikin harshen Fulatanci sune:

Malam Abdullahi Dan Fodiyo shakikin kanen Shehu Usmanu, Modibbo Wambe Andal, Muhammadu Bello Dan Shehu, Muhammadu Tukur Dan Binta, Mallam Ibrahim Halilu Dan Mallam Abdullahi, Abdulkadir Dan Mustapha Aliyu Babba Dan MUhammadu Bello, Saidu Dan Muhammadu Bello, Mallam Idrisu da sauransu.

A wajen almajiransa mata kuma akwai babbar diyarsa Khadijatu mahaifiyar shahararren malamin nan Mallam Abdulkadir Dan Mustafa; akwai kuma Fadimatu diyar Shehu matar Sarkin yaki Aliyu Jedo, kuma kakar waziri Ibrahim. Akwai kuma Hafsatu diyar Shehu matar Mallam Ibrahim Dembo Hamal na Birnin Gada da Fadimatu diyar Muhammadu Yero da kuma shaharrar diyar na ta Shehu Usmanu wato Nana Asma'u Uwar Gari matar Waziri Usman Gidado Dan Lema wadda take har kungiya ta kafa don koyar da matan birni da karkara addinin Musulunci wadda take har yanzu wannan kungiya na gudana akusan ko wane gari. Wannan kungiya ana kiranta "kungiyar 'yan Taru" [9]

## SASHEN RUBUCE-RUBUCEN FULATANCI A FANNONIN ILIMI DABAN-DABAN

Tarihi ya nuna cewa Shehu Usmanu da mataimakansa sun yi rubuce-rubucen fannonin ilimi daban-daban a cikin harsuna daban daban da dama, musamman a cikin harshen larabci, Fulatanci da kuma harshen Hausa. Hasali ma dai wasu littafan da shehu Usmanu ya rubuta a cikin larabci to ya wallafa wasu daga ciki sune cikin harshen Fulatanci, ko kuma ko kuma daga cikin almajiransa sun fassara su zuwa harshen Fulatanci kamar yadda ya ambata a cikin wakarsa ta Fulatanci mai suna <u>Yimre Mir'atu</u> a inda shike cewa:

> "Digoo mi wallifoo hi doo Ajamiyya hi fiiji dii digoo ba Arabiyya [10]

Ma'ana;

> Wanibi ina wallafawa cikin Ajami (Fulatanci/Hausa) wani bi kuma ina fassarawa cikin harshen Larabci

Haka kuma a cikin wata wa kasa ta Fulatanci mai suna <u>Yimre Joweji faa jowee,</u> yana cewa:

> "Amma fu tinnoroogimee Ajamiyyah Aahi bo balli faa di doo Arabiyyah"

Ma'ana; Jahillai suyi kokarin karatun wakokin ajami (Fulfulde/Hausa) Mallamai kuwa an wallafa musu su cikin Arabiyya"

A cikin daya daga cikin wakokinsa na Fulatanci mai suna Baabuwol kire Shehu Usmanu R.A ya fadi dalilin da yasa suke rubuce-rubuce a cikin ajami musamman a cikin harshen fulatanci a inda shike cewa akan baitoci na 4 da na 5 kamar haka:

" Nufaare de am yusbangue'en aabuwol kire mi yusbingol Fulfulde fullu fu yeetoyee".

Ma'ana; Nufina in wake babin Rafkannuwa (Babin Sahwu) in wakeshi cikin fulatanci masu jin fulatanci su jiya.

"to men jusbiri: Arabiyya Aalimi tan nan nani to men jusbirii Fulfulde Jaahili Faydoyee"

Ma'ana; Idan muka yi waka a cikin Arabiyya malamai kadai suka jiya, idan muka tsara a cikin fulatanci jahillai sai su unfana

Haka kuma jikansa Mallam Saidu dan Sarkin Musulmi Muhammadu Bello ya tabbata muna cewa, Shehu Usmanu ya zuba fannonin ilimi daban-daban a cikin wakokinsa na fulatanci wanda shike shine dalilin da yasa shi kansa Mallam Saidu ya rubuta waka akan Nahawun Fulatanci, a inda a cikinta shike cewa:

"Gam Shehu rootake Ande Koraihi Gimdi mu'u gaddoymi kaa'ida gam dolgoobe majji dalaa"

Kamin mu ci gaba da tsara fannonin ilimi da Shehu Usmanu R.A. ya rubuta a cikin harshen Fulatanci, ya kamata masu saurare su san cewa, harshen fulatanci shine harshen da Shehu Usmanu ya fara rubuce –rubuce a cikinsa. Kamar yadda wata waka ta Fulatanci daya rubuta mai tashi da Minoddiri Rahmanu ta bayyana muna a can karshenta. [13]

Ita wannan waka ya rubuta tana a cikin shekarar 1180 AH, a lokacin shina da shekaru 12 da haihuwa. Saboda haka muna iya cewa harshen fulatanci shine na farko da Shehu Usmanu ya fara rubuce-rubuce a cikinsa domin kuwa Mallam Abdullahi ya tabbata muna cewa wakar farko da Shehu Usmanu ya rubuta a cikin harshen larabci

it ace Ha li Masirun ta yabon Annabi Muhammadu SAW wadda ya rubuta a cikin shekarar 1188 AH a lokacin kuwa Shehu Usmanu na da shekaru 20 da haihuwa [14].

A bangaren rubuce-rubucen da yayi a cikin harshen Hausa har yanzu masu bincike basu binciko muna wadanda Shehu Usmanu ya rubuta kamin shekarar 1180 balle a gano cewa a cikin wane harshe ne ya fara rubuce-rubucensa, amma a bias binciken mai rubutu wannan takarda harshen Fulatanci ne kan gaba.

Wani abin lura kuma shine a karshen rayuwar Shehu Usmanu R.A., ba'a samu wani littafe ko waka day a rubuta a cikin harshen larabci ko Hausa ba, amma an samu rubuce-rubucen wakokinsa na fulatanci day a rubuta wadanda yake bayani a kan bayyanar Mahdi da kuma wadanda yak e bayani a kan cewa shi da jama'arsa duka Kadirawa ne. Wadanna wakokin duka ya rubuta su ne a cikin shekarar 1231 AH [15] a lokacin kuwa saura 'yan shekaru ko 'yan watanni shi rasu, domin masana tarihi sun tabbata muna cewa, Allah Yayi wa Shehu Usmanu rasuwa ranar litinin 3 ga watan Jimada Ahir na shekarar 1232 AH Allah shi yarda dashi shi kuma kara masa karama amin.

Hakika Shehu Usmanu R.A. ba fanning ilimin da bai tabo ba cikin rubuce rubucensa na fulatanci, kadan daga cikinsu sune.

1. **Fannin Ilimin Tauhidi:**

   A wannan fanni Shehu Usmanu yayi rubuce rubuce da dama a cikinsa. Daya daga cikin wakokin fulatanci day a rubuta a cikin wannan fanni it ace Yimre Asli Diina (Fannu Mo Tauhiidi) wadda a cikinta yayi bayani a kan wajabcin samuwar Ubangiji da sauran

bayanai a kan siffofinsa. Haka kuma yayi bayani akan Manzannin da Annabawa da abinda Allah Ya aikosu da shi.

2. **Fannin Ilimin Fasarar Alkur'ani Maigirma**

A wannan fanni Shehu Usmanu ya rubuta wakoki da dama a cikin harshen fulatanci. Daya daga cikin su it ace Kodol Zabarjadu ana kyautata zaton it ace kanensa Mallam Abdullahi ya fassara zuwa larabci yayi masa suna da Miftah Al Tafsir.

Shehu Usmanu ya rubuta wannan waka a cikin shekarar 1203 AH. Shi kuma Mallam Abdullahi a cikin shekarar 1209 AH.

3. **Fannin Li'irab**

Shehu Usmanu ya fassara matanin Ajaruma na Abi Abdullahi Muhammad Ajarum zuwa fulatanci a wake. Lamiyya ce amma ba'a samu ganinta ba lokacin da ake wannan bincike amma mai wannan binciken yasan akwaita a dakin karatun Alh. Junaidu Wazirin Sokoto.

4. **Fannin Ilimin Balaga**

A wannan fanni kuma Shehu Usmanu ya wallafa waka a kan wannan fanni yayi mata babi har 11 bayan muqaddima yayi ma wannan waka suna Yimre Dayal ana kyautata zaton littafin Bad'al Ma'ani wa Al Balagah ne ya fassara zuwa fulatanci. Ya rubuta wannan waka a cikin shekarar 1198 AH

5. **Fannin Ilimin Taurari**

A cikin wannan fanni Shehu Usmanu ya rubuta muna Yimre Sa'ada wadda a cikinta yayi muna bayanin kwanukkan shekarar ajami da kwanukkan shekarar Arabiyya. Ya fayyace muna

kwanukkan Shekarar Arabiyya 354 ta Ajamiyya kuwa 365. A cikinta kuma yayi muna lissafin kwanukan da rani kan yi da na damana, kaka da kuma na dari.

6. **Fannin Rabon gado**

A fanning rabon gado kuwa Shehu Usmanu ya rubuta muna Yimre Renoobe wadda a cikinta yayi muna bayanin yadda ake rabon gado, a inda ya faro tun daga dalilin dake sa ayi gado da rukunnan sa, sharuddansa da bayani a kan masu yin gado da kuma abinda ke hana ayi gado.

7. **Fannin Siyasa**

A wannan fanni, Shehu Usmanu ya rubuta muna Yimre Fiiji Laamu wadda a cikinta yayi muna bayani a kan wajabcin shugabanci da kuma nauoinsa, a inda yayi bayanin shugabancin Annabci, nag ado na limanci da kuma na shugabancin al'amurran yau da kullum na al'umma da kuma sauran bayanai da suka biyo baya.

8. **Fannin Ilimin Sufi**

A wannan fanni Shehu Usmanu ya rubuta muna Yimre Suufi wadda a cikinta yayi bayanin matakan da ake bi a zamo sufi

Wannan waka tana da fasulla har 14 kuma ya rubuta tare a shekarar 1201 AH.

9. **Fannin Tarihi**

A wannan fanni kuwa Shehu Usmanu ya rubuta muna wakoki da dama a kan tarihi daga cikinsu akwai Yimre Tsamiya wadda a cikinta yake bad a labarin abubuwan da suka gudana tsakanin sad a mutanen kasar Hausa da kuma sarakunansu sa'adda ya fara wa'azi tun daga farko har zuwa lokacin da Allah ya bashi nasara a kansu.

## ILLOLIN DA KE CIKIN RASHIN BINCIKEN RUBUCE-RUBUCEN FULATANCI NA SHEHU USMANU DA MATAIMAKANSA A WAJEN RUBUTA TARIHI KO GUDUMMUWARSU A DAULAR USMANIYYA

Marubuta tarihi da dama suna ko oho da rubuce-rubucen ajami na Shehu Usmanu da mataimakansa wajan rubuta tarihi ko gudummuwarsu basu kula da cewa mafi yawan rubuce-rubucensu duk a cikin Ajami suka yisu suka kuma yi bayani kwatta-kwatta saboda yawan jahillai a wancan lokaci nasu don haka duk cikakken bayani mai saukin fahimta shina cikin rubuce-rubucensu na ajami. Rubuce-rubucen da suka yi cikin Arabiyya don malammai kawai suka yisu ba don jahillai ba [17], saboda haka binciken wadannan rubuce-rubucen na ajami yana da muhimmaci kwaran gasket a wajen rubuta tarihi ko gudummuwar wadannan bayin Allah.

A gain mai rubuta wannan takarda wadannan masu dogara kashi daya bias ukku na sashen rubuce-rubucen magabatanmu kuma su yanke hujja a kan wasu al'amurran magabatanmu ba tare da amfani da sauran sasheba, to bas u yi ma magabatanmu adilci ba, domin shikan yiwu sufi bada gudummuwa ko bayani a cikin wadancan harsuna da ba'a bincika ba fiye da harshen da aka yi bincike cikinsa shi yassa da yawa ake ganin wallen irin wadannan marubuta saboda irin tuba-tuban da za'a gain a cikin rubuce-rubucensu.

Misalan irin wadannan tuba-tubai ana iya ganinsu a cikin <u>Al mutali'at Al Wadihah Li Al Madaris Al Wadilah Li al Madaris Al Thanawiyyah Al Kubra Al Najeria</u> na Bashir Ahmad Muhyiddini da Muktari a kan Shehu Usmanu R.A. ya tafi Makka yayi karatun Addinin Musulunci a can sa'adda ya zama malami sannan ya komo gida (Degel) wanda shike ba gaskiya neba. Da ace wadannan marubuta sun karanci wakar

Fulatanci ta Nana Asma'u diyar Shehu mai suna Khabaruuji Shehu da sun ga wuraren da Shehu yayi karatu da kuma garuruwan daya tafi tun daga haifuwarsa har zuwa rasuwarsa.

Haka kuma a cikin Tarikh Sokoto na Hajj Sa'id akan shafi na 189 ya ambaci cewa lokacin da Shehu Usmanu ya rasu an yi ma Muhammadu Bello mubaya'a a cikin gidan Abubakar Dan Jada.

Wannan takarda ta bayyana muna irin rawar da harshen fulatanci ya taka a wajen jaddada Addinin Musulunci da fannonin ilimi daban-daban a kasar nan tamu ta Hausa. Haka kuma ta bayyana muna cewa Fulani sun fitone daga zuriyar Uqbatu Ibn Naf'I a sakamakon auren da yayi da Bajjo Mangu suka haifi yaya hudu.

Haka nan kuma wannan takarda ta bayyana muna yadda halayen mutanen kasar Hausa suke kamin bayyanar Shehu Usmanu mun kuma ga irin hanyar da Shehu Usmanu ya bi ya tarbiyyantarda almajiransa hanyoyin da zasu bi su risbe miyagun al'adun kasar Hausa, tare da bada sunayen wasu daga cikin almajiransa da suka taimaka ta fanning rubuce-rubucen wakokin wa'azi da fannonin ilimi daban a cikin harshen fulatanci, mun kuma ga dalilan da suka bayar na rubutawa a cikin wannan harshen har wayau dai wannan takarda ta bayyana muna cewa wanann harshe ne na fulatanci Shehu Usmanu ya fara rubuce-rubuce a cikinsa haka kuma da shine kuma yayi rubuce-rubuce a karshen rayuwarsa wato a shekarar 1231 AH domin ya rasu a shekarar 1232 AH.

Har wayau dai wannan takarda ta tsaro muna kadan daga cikin rubuce-rubucen da Shehu Usmanu yayi cikin harshen fulattanci a kan

fannonin ilimi daban daban. Sa'annan daga karshe ta bayyana muna kadan daga cikin illolin rashin binciken rubuce rubucen da shehu Usmanu R.A da mataimakansa suka yi a cikin Ajami musamman wadanda suka yi a cikin harshen Fulatanci.

**HASHIYA**

1. Alh. Abubakar Wazirin Kano ; Kano ta Dabo ci Gari shafi na 33.
2. Muhammadu Makwashe b. Umar; Tarihin Ajamin,
   Tarihin mujaddadi shehu Usmanu shafi na 1.
3. Alh. Dr. Junaidu Wazirin Sokoto ; Tarihin Fulani shafi na 1-2.
4. Shehu Usmanu B. Fodiyo: Yimre Moodinoore shafi na 1
   a kan bai na 5-9.
5. Sidi Sayudi Muhammad da Jean Boyd:
   Fassarar, Infak-Al Maisur shafi na 3-4.
6. Shehu Usman B. Fodiyo: Yimre Tsamiya shafi na 7-8
   akan baiti na 50-65.
7. Dubi wakar da aka ambata a sama akan baiti na 49.
8. Misali wakar shehu Usmanu Yaynatoode (Boneeji lesdi Hausa)
9. Wadannan Malammai da aka ambata dukansu sun rubuta wakokin wa'azi da fannonin Ilimi daban-daban a cikin harshen fulatanci.
10. Dubi Yimre Mir'atu ta Shehu Usman akan baiti na 19 idan faro kida daga karshenta.
11. Shehu Usmanu B. Fodiyo; Yimre Joweeji faa Jowee akan shafi na 2 baiti na 17.
12. Saidu B. Bello ; Yinire fannu Nahawu akan shsfi na 1 baiti na 4.
13. Shehu Usmanu B. Fodiyo; Yinire Minodduri Rahmanu akan baiti na 11.
14. Abdullahi B. Fodiyo; Tazyin Al waraqat shafi na 8-10

15. Shehu Usman B. Fodiyo; Yimire Bangaare Maadi yinire mahdi akan baiti na 48.
16. Usman Gidado B. Laima; Raud Al Janan akan shafi na 85.
17. Shehu Usman B. Fodiyo; Yinire Baabuwol kire akan baiti na 4-5.
18. Asma'u B. Shehu U. Fodiyo; Yinire Habaruuji Shehu akan baiti na 110 – 111.
19. Dubi wakokin A sma'u B. Shehu Usman da aka ambata a sama akan baiti na 113 – 114.

## MADOGARA; LITTAFFAN LARABCI.


1. Abdullahi B. Fodiyo: Miftah Al Tafsir, Zaria.
2. Abdullahi B. Fodiyo: Tazyin Al Waraqat, Sokoto, Rabiul Awwal, 1383 A.H.
3. Abdulkadir B. Gidado; Anis Al Mufid, rubutun hannu (Foto) a dakin littaffan Ibrahim Junaidu Sokoto.
4. Usman Gidado B. Laima; Raud Al Jinan fi dhikr ba'ad manaqib Alshaykh Uthman b. Foduye, Kano.
5. Waziri Junaidu; Al Risalat Al Nasihat Li Muwalliat Al-Mutali'at Al Wadihat, Sokoto.
6. Waziri Junaidu; Kitab Zikr Al Amakin Allati Makatha fiha Alshaykh Uthman, foton rubutun hannu a dakin littaffan Ibrahim Junaidu Sokoto.

**MADOGARA LITTAFFAN FULATANCI**

7. Abubakar B. Muhammad; Gime Fulfulde de Sheekhu Usmaanu Bii Foodiye E wodbe moodibbe, center for the study of Nigerian Language, Bayero University, Kano, 1993.
8. Nuhu Umar Jalingo; Gime Nana Asma'u E De Wobbe, Jamiar Bayero kano, 1994.
9. Waziri Junaidu; Diiwaanu Gime Fulfulde de Sheehu Usmanu, Abdullahi bibbi Foduye E de wodbebibbe Mabbe E Worbe E de E Rewbe E de wodbe Moodibbe; rubutun hannu a dakin littaffan Waziri Junaidu.

**MADOGARAR LITTAFFAN HAUSA**

10. Alh. Abubakar Dokaji Kano: kano ta Dabo ci Gari, (bugawa ta biyu) Zaria, 1978.
11. Aliyu Muhammad Makwashe: Tarihin Ajami, Tarihin
12. Mujaddadi Ssmanu tare da sarakunan Musulunci, Gusau, 1406 AH.
13. Ibrahim Imam: Tarihin Mujaddadi Shehu Usmanu Dan Fodiyo, Zaria, 1966.
14. Sidi Sayudi Jean Boyd : Fassara a takaice ta littafan Infaq Al Maisur Na Sarkin Musulmin Muhammadu Bello, Zaria, 1974.
15. Waziri Junaidu: Tarihin Fulani, 1959, Zaria Madogara: Littafian Turanci
16. Al-Amin Abu Manga: Directions for Research on Fulfulde and Fulbe culture, Jamiar Bayero Kano, 1982.
17. A. Mukoshy: A Fulfulde English Dictionary Kaduna, 1991.

18. S.J. Hogben: An Introduction to the History of the Islamic States of Northern Nigeria, Ibadan 1967.
19. J. Boyd & Beverley B. Mack: The collected works of Nana Asma'u Daughter of Usman Dan Fodio, Ibadan, 1999.
20. H.A.S. Johnston : The Fulani Empire of Sokoto London, 1967.
21. Murray Last: The Sokoto Caliphate, Bristol, 1967.